# Lallai cewa Manzon Allah-Tsira da Amincin Allah su tabbata a garesu- "cewa lallai Annabi ya hana cin kudin kare, Da Sadakin karuwanci, da kuma ladan boka".

Daga Dan Mas'ud-Allah ya yarda da shi- : "cewa lallai Annabi ya hana cin kudin kare, Da Sadakin karuwanci, da kuma ladan boka".
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Hanyoyin neman Arziki na Halak suna da yawa, kuma Allah ya sanya su a maimakon wasu Munanan hanyoyiwadanda basu da Albarka, to yayin da hanyoyin farko ta wadatar da Mutum ga barin hanyoyin na biyun, kuma da kasancewa hanyoyin na biyun barnarsu ta girmama kuma babu wani amfani da yake biye da shi, sai Shariah ta Haramta miyagun hanyoyin baki daya, wadan nan sunehanyoyi Ukun: 1.Sai da Kare: don shi Najasa ne kuma kazanta ne. 2.kuma da abinda karuwa ta karba na ladan fajircinta, wanda da shi take bata Duniyarta da Lahirarta. 3.Kwatankwacinsa abinda Boka da 'Yan Bori da Masu batar da Mutane, daga cikin wadanda suke Da'awar Gaibu da kuma iko kan dukkan Halittu, suke damfarar Mutane -Da Karyarsu- don su wawashe musu Dukiyoyinsu, sai su ci dukiyar ta hanyar barna, kuma dukkan wadan nan hanyoyi sun munana kuma sun haramta, kuma bai halatta a aikata su, haka kuma bada wani lada akansu, kuma Allah ya canza musu da Mafi Alkairi halattacce kuma mai tsafta.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/6036